# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na biyar: Don mu baƙar fata ne?

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | 'yar shekara 20 |
| Mai shela a filin jirgi: | 'yar shekara 35 |
| Jami'in tsaro: | ɗan shekara 40 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Suleman: | ɗan shekara 19 |
| Hamid: | ɗan shekara 60 |
| Sa'adatu: | 'yar shekara 35 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |

Jami'an tsaron kan iyakar teku: ɗan shekara 40

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. Wannan shi ne kashi na biyar na wasan kwaikwayonmu mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai”. A ƙarshen shirin da ya gabata mun ji yadda Faisal ya samo wata dabarar haurawa zuwa Turai ta hanyar amfani da wani kwale-kwale mallakar mahaifin abokinsa Suleman, wanda da ma shi masunci ne tsawon rayuwarsa. Can kuma a ɗaya ɓangaren mun ji halin da Lami ta shiga a wata *airport* a kan hanyarta ta zuwa garin da jami’ar da za ta yi karatu take.

Yanzu sai ku gyara zama don jin yadda za ta kasance a cikin kashin namu na yau mai suna “Don mu baƙar fata ne?”. Da farko za mu fara ne ta inda Lami ta zo wucewa ta ƙofar da jami’an tsaro suka sa na’urar binciken fasinjoji.

**Fitowa ta 1: Lami a ƙofar jami’an tsaro**

**Jami’in tsaro:** ’Yammata, sake komawa baya ki fito da dukkanin abubuwan da ke cikin jakarki waɗanda suka shafi ƙarfe, kamar zobe ko abin wuya ko kuma kuɗi...

**Mai shela:** Kira na ƙarshe ga Malama Lami Talle! Malama Lami Talle kina ina, jirgi fa ya cika. Ki yi maza ki biyo ƙofa ta biyar ko kuma mu sauke kayanki.

**Lami:** Ranki ya ɗade, ni ce… Wallahi, ni ce, sunana ake kira!

**Jami’in tsaro:** To ba sai ki tafi ba, me kuma kike jira? Tafi mana!

**Lami:** Wayyo Allah, na shiga uku! Allah ka sa kar jirgin nan ya tafi ya bar ni. Ban san ida zan sa kaina ba!

**Mai ba da labari:**
Nan da nan sai Lami ta tattara 'yan komatsanta cikin sauri ta garzaya zuwa ƙofar da za ta hau jirgin. Allah dai ya amsa addu'arta domin kuwa ta samu isa wajen jirgin a kan lokaci. To, ko wa kuke tsammanin za ta gani a kusa da kujerarta daga zamanta. Ai ba wata ba ce sai Sa'adatu. Duk sai ta ji ta sami sauƙi. Sai dai kuma kafin mu ji abin da Sa'adatu za ta ce, yana da kyau mu koma wajen Faisal da abokinsa Suleman a can gaɓar teku inda a yanzu haka suke shaida wa baban Suleman, wato Malam Hamid, irin shirin da suka yi.

**Fitowa ta 2: Faisal da Suleman suna magana da baban Suleman, Malam Hamid**

**Faisal:** Kana ji ko Baba, ina ganin wannan ba wani abin damuwa ba ne. Da zarar mun isa Turai kuma mun fara aiki za mu sayo maka sabon kwale-kwale mai inji, wanda ya fi naka ma, kuma za ka iya barcinka ko da ana ruwa. Ai ka gane wanda nake faɗa ko?

**Hamid:** Lallai Suleman yau na san kai da wannan abokin naka ba ku da kunya! Wai har ma ni za ku zo ku same ni da maganar na bayar da abin da da shi kaɗai na mallaka a duniyar nan wajen neman abincin da zan ci ni da iyalina? Ni dalilin ma da kuka ba ni ya fi komai takaici. Wai don za ku tafi garin Bature. Ni na rasa abin da matasa suke gani a ƙasashen nan na Turawa.

**Suleman:** Faisal, ka ga da ma abin da nake gaya maka. Na gaya maka in dai babana ne, wannan dabarar taka ba za ta taɓa samun shiga a wurinshi ba.

**Hamid:** Wato ina magana kana magana ko? Saboda tsabar rashin tarbiyya ko? Da ma wannan shi ne irin abin da kuke koya

daga gun Turawa ko? To, ku karkaɗe kunnuwanku ku ji. Tun ina ɗan shekara sha biyar nake kamun kifi. Don haka ban ɗauki sana'ata da wasa ba, kuma ban ɗauki wannan kwale-kwalen nawa abin wasa ba! Ku ɓace min da gani, mutanen banza!

**Faisal:** Wallahi Baba, da za ka ɗan tsaya ka ji dalilin da ya sa muke so…

**Hamid:** Idan ba ku ɓace min da gani ba, kowa jikinsa zai gaya masa. Maimakon ku je ku nemi aikin yi, kuma ku nemi matan da za ku aura su haifa muku 'ya'ya, sai kawai ku tsaya kuna ɓata lokacinku a kan mafarkin zuwa Turai, da rana tsaka.

**Faisal:** Mafarki ne ma? Haba Baba, wannan ai ya fi ƙarfin mafarki.

**Mai ba da labari:**
Yanzu dai ga Faisal can ya bar wajen baban Suleman a gaɓar teku. Ko da yake ransa ba a ɓace yake ba, amma kuma gwiwarsa ta yi sanyi. To ko wannan shi ne ƙarshen mafarkin da ya sha yi na tafiya Turai? Yanzu bari mu juya wajen Lami da Sa'adatu a yayin da suka isa garin da za su je bayan 'yar tafiyar da suka yi a cikin jirgi. Dole sai da Lami ta sake fuskantar wani babban binciken daga jami'an shige-da-fice, kafin a bar ta ta shiga cikin ƙasar. Yanzu dai ga shi can ta samu isa inda za ta. Ga kuma Sa'adatu yanzu ta gayyace ta don su sha shayi.

**Fitowa ta 3: Lami da Sa'adatu suna shan shayi a *airport* ɗin Turai**

**Lami:** Wallahi Sa'adatu, ban taɓa tsammanin zan sha wahalar da na sha ba. Gaskiya na ji jiki. Ban taɓa tsammanin haka abin

yake ba. Sai ki ga kowa ba ya haba-haba da mutane, kamar ba wanda ya amince min, balle ma ya so yi magana da ni.

**Sa'adatu:** Ai yanzu kika san kin shigo Turai. Ba ki sani ba, ina da wata ƙawa wadda takan ce "Launin fatata ne ya jawo min".

**Lami:** Me take nufi da hakan?

**Sa'adatu:** Abin da take nufi shi ne, wai saboda launin fatarmu shi ya sa ake wahalar da mu a nan haka. Amma kuma na san cewa ba kowa ne a wannan ƙasar yake nuna wariyar launin fata ba. Domin kuwa da haka ne da ban auri Bature ba! Gaskiya na tausaya miki yadda kika sha wahala a zuwanki na farko wannan ƙasar. Ina ganin dalilin da ya sa shi ne: mutane a nan sun riga sun tsorata da barazanar ta'addanci. Kuma ko ba haka ba, da ma mutanen nan ƙasar ba su da haba-haba da mutane kamar yadda mutanen ƙasashenmu na Afirka suke da shi. Sai dai ki daure ki saba da haka.

**Lami:** Sa'a, na gode da wannan shawarar da kika ba ni. Don Allah kar ki ce na zaƙe, ko zan iya amfani da wayarki? So nake na yi wa iyayena saƙo cewa na sauka lafiya, domin na san duk yanzu suna can cikin damuwa.

**Sa'adatu:** Haba, ba komai mana, ɗauki kawai ki kira su. Za su ji daɗi idan suka ji muryarki.

**Lami:** Na ko gode, Sa'a. Gaskiya kina da kirki.

**Sa'adatu:** Ba kome, na gode.

**Malam Talle:** Alo? Wa ke magana?

**Lami:** Baba! Ni ce, Lami.

**Malam Talle:** Lami! Allah na gode maka. Yaya kike? Kin sauka lafiya?

**Lami:** Ina nan lafiya ƙalau Baba.

**Malam Talle:** Da wace lamba kike kirana?

**Lami:** Wannan lambar wata ƙawata ce. Gaskiya dai na sha wahala, kuma na kusa rasa jirgina na biyu. Ga shi kuma mutanen garin sam ba su da kirki. Amma fa Baba, Turai ta ba ni sha'awa.

**Malam Talle:** Alo? Lami! Kai, ba na jin ki sosai. Daga ina kike kirana ne?

**Lami:** Baba, ka yi haƙuri, sai an jima. Ka gaya wa Mama na sauka lafiya. … Na gode Sa'a. Wallahi na san hankalin iyayena yanzu zai kwanta da suka ji na sauka lafiya.

**Sa'adatu:** Haka ne kuwa. Yauwa Lami, bari na ba ki wata shawara. Kada ki kuskura nan gaba ki faɗa wa mutan gida cewa kina wahala a nan Turai. Kina jina? Ko wane irin halin kika shiga, kar ki gaya musu gaskiya!

**Lami:** Ban gane ba! To, saboda me kuwa Sa'a? Su fa iyayena ne, kuma wajibi ne su san halin da nake ciki!

**Sa'adatu:** Mmm… Gaskiya Lami, ba sai na gaya miki dalili ba. Ke dai kar ki manta da abin da na gaya miki! Wata rana za ki gano dalilin da ya sa na gaya miki haka. … O, bari na tafi. Ga direba can ya zo. Yauwa, karɓi wannan Yuro ashirin ɗin ki

biya kuɗin shayin da muka sha. Sai ki riƙe canji.

**Lami:** Na gode.

**Sa'adatu:** Yauwa. Kar dai ki manta da lambata. Kya iya kirana idan kina buƙatar taimako. Gaskiya na ji daɗin haɗuwa da ke. Bari in tafi. Sai an jima, kuma ki dinga kula, kin ji? To, sai wata rana.

**Lami:** To, sai wata rana. Na gode. Sai an jima.

**Mai ba da labari:**
Ga Lami nan dai ta zuba wa Sa'adatu ido yayin da take tura jakukunanta zuwa filin fakin ɗin motoci. Yanzu bari mu rabu da batun Lami haka nan a yayin da ta shiga sabuwar rayuwa. Bari mu koma wajen Faisal don mu ji halin da yake ciki a can Afirka ta Arewa. Idan kuna biye da mu, bayan da baban abokinsa Suleman ya ƙi ya ba shi aron kwale-kwalensa, sai Faisal ya yanke shawarar bin wasu 'yan gudun hijira da ke ƙoƙarin tsallakawa zuwa Turai a cikin wani ɗan ƙaramin kwale-kwale. Amma fa babu wanda ya gaya wa wannan shawara da ya yanke, ko da kuwa da babban abokinsa Suleman. Bayan da waɗannan 'yan gudun hijra suka shafe kwana da kwanaki suna tafiya a cikin teku, yanzu dai ga Faisal can shi da abokan tafiyarsa sauransu 'yan kilomita kaɗan zuwa gaɓar Turai.

**Fitowa ta 4: Karan batta tsakanin jami'an tsaron kan iyakar teku da 'yan gudun hijira ta ɓarauniyar hanya**

**Jami'an tsaron kan iyakar teku:** Ku saurara. Mu ne jami'an tsaron gaɓar tekun Turai. Kowa ya kwantar da hankalinsa! Kada wanda ya ce zai faɗa ruwa! Jami'anmu za su yi muku jagora.

| | |
|---|---|
| **Faisal:** | Ina za ku kai mu? Mu so muke mu tafi Turai. Mun san mun kusa isa, ga shi ma mun fara hango gaɓarta. |
| **Jami'an tsaro:** | Mun kama wannan kwale-kwalen naku ne a iyakar tekun Afirka, don haka za mu mayar da ku can da zarar mun gane daga inda kuka fito. |
| **Faisal:** | Ai mu ba so muke mu koma ba. Mu ba mu da wasu takardun shaidar inda muka fito. Mu ba 'yan kowace ƙasa ba ne! |
| **Jami'an tsaro:** | Ba komai, za dai mu ga yadda za a yi. Ni abin da idona ya nuna min shi ne kuna ƙoƙarin tasallakawa zuwa Turai ba bisa ƙa'ida ba. Mu kuma aikinmu shi ne mu tabbata mun kare iyakokinmu. Don haka muna so ku ba wa jami'anmu haɗin kai idan kuna son zaman lafiya. |
| **Faisal:** | Ni wallahi ba inda zan koma! Ni ba zan koma ko'ina ba! Babu wanda ya isa ya mai da ni baya! |
| **Jami'an tsaro:** | Ga shi can ya faɗa ruwa. Ku yi maza ku fito da shi, kada igiyar ruwa ta ja shi, don tana da ƙarfi! |
| **Faisal:** | Habu… Habu… |
| **Jami'an tsaro:** | Ka same shi? Yaya yake? ... Yauwa. Kai! Duk ku tsaya ku ji! Ba ma son wani abu ya samu wani daga cikinku. Don haka kowa ya kwantar da hankalinsa, ya zauna a cikin wannan kwale-kwalen. Idan kun yi haka, ba abin da zai same ku… |

**Mai gabatarwa:**

Yanzu dai jami'an kula da gaɓar tekun Turai sun ceto Faisal daga cikin teku.

Ga shi can kuma an tasa ƙeyarsa zuwa Afirka ba da son ransa ba. Amma fa kuma duk da haka yana nan a kan bakansa na tsallakawa zuwa Turai. Ko wace dabara zai fito da ita kuma nan gaba? Sai ku kasance da mu a wani shirin don mu ji yadda za ta kasance.

A nan kuma muka zo ƙarshen wannan kashin, na shirin wasan kwaikwaiyonmu mai taken "Tudun mun tsira – Mai Bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". Ku kasance da mu a kashi na gaba don ku ji yadda Lami za ta fuskanci karatunta a Turai. Kuna iya kuma kasancewa da mu ta shafinu na tattaunwa da ke facebook.com/dw.lbe. Ku huta lafiya!